Kada ku hana bayin Allah mata (zuwa) masallatan Allah, saidai su fita alhali ba su yi mummunar shiga ba

Daga Abu Huraira Allah - Ya yarda da shi - cewa Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ya ce: «Kada ku hana bayin Allah mata (zuwa) masallatan Allah, saidai su fita alhali ba su yi mummunar shiga ba».

[Hasan ne] [Abu Dawud ne Ya Rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya hana majiɓincin al'amarin mace da wanda ke kula da ita game da hana mata zuwa masallatai, kuma ya umarci mata in zasu fita su fita ba tare da sun shafa tirare ba, kuma ba tare da sun yi mummunar shiga ba; dan kar su zama sababi a fitinar maza.

https://sunnah.global/hadeeth/ha/show/65416